BU African Studies Center LANGUAGE PROGRAM, 232 BAY STATE ROAD, BOSTON, MA 02215 africa@bu.edu
www.bu.edu/Africa/alp 617.353.3673

## Skit 4: Ƙaiƙai koma kan masheƙiya

| | |
|---|---|
| **Yazi Dogo:** | **Mugunta dai ba ta da ƙyau balantana yinta. Kar ka yi abinda bai da ƙyau dan wata rana zai komo ma.** |
| Ɗan Barno (ƊB): | To, ke ni hwa zani huta. |
| A2: | Ɗan Barno, tun da sahe? |
| ƊB: | To ƙaƙa kike so? Mi zani zamnawa in yi a cikin gida? |
| A2: | Haba Dan Barno? Ka bari ko wasu diya naka su tashi su ganeka da kwana. |
| ƊB: | A mi zani yi? Abinda ba ni da abin basu! Ni ba ma dan su ba dan mai gidan ne zani hita. Don ban son ya tardo ni ya yi mini **walaƙanci**, bani da kuɗin biyanshi. |
| A2: | Yau Ɗan Barno, ka bari mai gida ya ganeka. |
| ƊB: | A'a. |
| A2: | Mai gida in ya zo ba sai ka san abinda zaka hwaɗa mishi ba? |
| ƊB: | Mi zani hwaɗa mishi? Mai gida, kuɗi yake so ba ni da kuɗin ba shi in kina da kuɗin ba shi, in zamna in ya zo a ba shi, in ba ki da kuɗin ba shi ki bar ni in tai in nema. In zamna haka nan ... |
| A2: | In ina da kuɗi Ɗan Barno ba ka gaya min haka. |
| ƊB: | To I haƙuri in zo. |
| A2: | Matsalar, yanzu ni za a like ma ɗaki |
| ƊB: | To, I haƙuri. I haƙuri in je in dawo! |
| A2: | E! Allah! Yanzu matsalar ni za a liƙe ma ɗaki. Da |

© Boston University

| | |
|---|---|
| | mai gida ya bi ka **kuɗin haya**, mace ta a da larura! Tun da maceta za a liƙe ma dan abin da muke samu muna kwanci. To, babu kamar Allah! Bari in shiga in gani in sun tashi in sami ko ɗan **ƙamzo** in **gwaɓa** musu. |
| A3: | Inda ma na ganshi! He, maƙwabci! Muna lahiya? |
| ƊB: | Lahiya lau wallahi? |
| A3: | Kai! An yi kwanaki ban gane ka ba, lahiya? |
| ƊB: | **Sabko**n hita nan da ka ga ina yi ai mai gidan ne nake wa gudu kar ya zo ya ritse ni ba ni da kuɗin biya, ya yi min tonon asiri. |
| A3: | E. Akwai zancenka. Amma in dai ana gamuwa ana hira ana tattamnawa ba a rasa dubarar da an kai. |
| ƊB: | To. |
| A3: | Yau kuɗin nawa ne? |
| ƊB: | Kai **da dama**. |
| A3: | Sun kai jimillar nawa? |
| ƊB: | Wallahi ... jika ɗari da ashirin ne. |
| A3: | Yanzu sabo da jika ɗari da ashirin dai ne kawai ka hana ma iyalinka jin daɗi ba ka tsayawa suna ganinka. |
| ƊB: | Ni gare ni da yawa ne. |
| A3: | To diba, **kwantad da** hankalinka. Ba dai jika |

| | |
|---|---|
| | ɗari da ashirin ne ba? Mai sauƙi na. Yanzu ka je wajen Alhaji ina samunka. Bari in shiga cikin gida in hito. |
| ƊB: | Ka biya? |
| A3: | Je ka kawai in same ka! |
| ƊB: | Allah ya sa albarka, na gode. Madalla. |
| A3: | Na shiga cikin ɗakina in hito. E! |
| ƊB: | A'a, bari ni ma in tahi can wurinshi yanzu can zani. Can zani. |
| ƊB: | Salamu alaikum! |
| Alhaji: | E... Yahaya? |
| ƊB: | Alhaji, Barka da kwana. |
| Alhaji: | Muna lahiya Ɗan Barno? |
| ƊB: | Lahiya lau. |
| Alhaji: | Ina gida? |
| ƊB: | Alhamdulillahi. |
| Alhaji: | Yara duk lahiya lau? |
| ƊB: | An tashi lahiya? Lahiya lau, wallahi. |
| Alhaji: | Mun kwan biyu ba mu haɗu ba. |
| ƊB: | To. Harakar ce, sai a hankali, sai a hankali. |
| Alhaji: | Ka kwantad da hankalinka. |
| ƊB: | Sai a hankali, sai a hankali. |
| Alhaji: | Na ji labarin an ce sabko kake yi ka huta. |
| ƊB: | To garin ne. Garin ne ... |

| | |
|---|---|
| Alhaji: | Shi ba komi ba ne harakar duniya. |
| ƊB: | Garin ne, garin ne zaman gidan ba ya yi. Yanzu ma ni da Kalla ne muka **yi shawara**. Shi ma yana nan tahe. |
| Alhaji: | A, to madalla. |
| ƊB: | E. Yana nan tahe. |
| Alhaji: | Madalla! |
| ƊB: | Kalla! |
| Kalla: | Aa! Ina zuwa! |
| ƊB: | Zo manna, kai muke jira! |
| Kalla: | Na'am! |
| ƊB: | Yau, kai muna jiranka! |
| Kalla: | Ina zauke. Salamu alaikum! |
| Alhaji: | Kai! |